# SUNNAH NEWS NIGERIA

Labaran Sunnah A Tafin Hannun ku

**MUJALLAR SUNNAH DOMIN SANIN HALIN DA SUNNAH KE CIKI**

*DATE: Friday 12, January, 2018*

## TSOHON MAI BAIWA GWAMNAN TARABA SHAWARA YA MUSULUNTA

### Wata Yar Wasan Kwaikwayo Ta Kudancin Nigeria Ta Musulunta

Liz Anjorin day ace daga cikin fitattun 'yan wasan kwaikwayo na kudancin kasar nan wato (Nollywood), wadda a yanzu haka ta karbi addinin musulunci inda ta shaidawa majiyar Sunnah News dalilin da yasa ta karbi addinin na musulunci, Liz Anjorin tace hakika wani musulmi shine yayi sanadiyar musuluntarta bayan wayar da kanta da ya dinga yi kan hakikanin addinin musulunci.

Addinin musulunci dai yana cigaba da samun karbuwa a yankuna daban-daban na duniya ko yaushe ana samun karuwar masu shigowa cikin addini,
A tarayyar turai ma yanzu haka masana sun tabbatar da cewa ana hasashen kara samun rubanyawar masu gangamin shiga addinin saboda kyawawan dabi'u da addinin yazo dashi, Allah ya taimaki musulunci da musulmai Amin,
Rahoto: *Basheer Sharfadi*

Tsohon mai baiwa gwamnan Taraba shawara kan harkokin siyasa, Mista Adamu Kwanci ya karbi musulunci.

Mista Kwanci ya ce bai yanke shawarar shiga addinin Musulunci ba sai da ya gudanar da bincike da dogon nazari, sannan karshen lamari ya gane cewar Musulunci shine Addinin gaskiya, sannan Musulmi sune jama'ar da su ka fi kowa son zama lafiya da tausayi.



Mista Adamu Kwanci wanda a yanzu ya sauya suna zuwa Malam Adamu Muhammad Kwanci ya karbi kalmar shahada ne daga wajen Babban Malamin Addinin Musulunci nan mazaunin garin Jalingo Dakta Ibrahim Jalo Jalingo. Sannan ya yi alkawarin zama jakadan Musulmi wajen wayar wa Kiristocin Jihar Taraba kai akan gaskiyar Musulunci da Musulmi, su gane karya da sharri da ake yi wa Musulmi a jihar da Nijeriya dama duniya baki daya.

Rahoto: **Hussain Auwalu Ya'u**

**Sabuwar Tashar Sunnah News TV Tana Kan Hanya**

**A yanzu** dai tuni dandalin Sunnah News yayi nisa wajen samar muku da sabuwar tashar talabijin wadda zaku iya samu a wayoyin ku, ana saran fitowarta cikin mako mai zuwa.

**Darulfirk.com Takuce Domin Yada Sunnah**
**Cibiya guda daya tilo wadda take kawo muku karatuttukan maluman Sunnah daga wurare daban-daban a kowane lokaci, aciki da wajen kasarmu Nigeria.**

**http://facebook.com/darulfikrng**

## KU DAINA KIRAN MUSIBAR NUMAN DA CEWA RIKICIN KABILANCI Dr- Ibrahim Jalo Jalingo

1. Ku daina kiran musibar Numan da cewa rikici ne na kabilanci; watau rikici ne da yake tsakanin Kabilar Fulani da Bachama, ko Fulani da Tiv, ko Fulani da Jukun, ko Fulani da Nyandag, ko Fulani da Mumuye, ko Fulani da .....
2. Gaskiyan wannan al'amari shi ne: wannan musibar sakamako ne na irin tasirantuwa da Kiristoci suka yi ne da tarbiyyar da Kungiyar CAN take cusa musu na nuna kiyayya da gaba da tsongwama ga al'ummar Musulmi a duk inda suke, kuma ko da daga wace Kabila ne suka fito. Mummunar tarbiyyar da take cusa musu na cewa: constitution din Nigeria an yi shi ne domin fa'idantar al'ummar Kirista kawai, amma banda al'ummar Musulmi!!
3. Saboda haka dukkan Kiristan da ya tasirantu da wannan muguwar tarbiyya ta nuna kiyayya da gaba; sawaa'un Bachama ne shi, ko Nyandang, ko Bahaushe, ko Babarbare, ko Bafillace, ko Mumuye, ko Tangale, ko Igbo, ko Bayarbe, ko Tiv, ko Jukun, koma wanene ne shi Wannan shi ne matsayinsa; Watau kashe Musulmi da kona dukiyarsa, da raba shi da dukkan wani hakki nasa a duk lokacin da ya sami damar yin hakan.
4. Azzalumar dokar hana wa al'ummar Fulani musulmi kiwon shanunsu kamar yadda suka saba yi cikin dazukan Nigeria tun shekaru mara iyaka da suka wuce, da gwamnan Jihar Benue Kirista ya kafa, da kuma gwamnan Jihar Taraba Kirista shi ma ya kafa Lalle bangare ne na tasirantuwa da wannan muguwar tarbiyya da Kungiyar CAN take yi wa kiristocin Nigeria domin share al'ummar Musulmi daga dukkan wani muhimmin hakki nasu.
5. Wannan shi ne hakikanin yadda al'amarin yake; saboda haka ya kamata yan'uwa su fahimci haka su daina biye wa farfagandar Turawa wacce ake ginawa cikin mafi yawan lokuta a kan nunawa al'ummar Musulmi wariya, a duk lokacin da abin ya shafe su tare da wasu al'ummar Kirista, ko al'ummar yahudu.
6. Allah muke roko da Ya tausaya mana Ya hada kawunan yan kasarmu ta yadda za su fahimci cewa ba za mu iya gina kasarmu da al'ummarmu ba ta irin wannan hanya ta neman share wata Al'umma daga dukkan wani muhimman hakki nata. Ameen.

*Rahoto: **Basheer Sharfadi***

## DAGA MASALLATAN JUMU'AR MU

**Shiri ne dake kawo muku jigon sakonnin hudubobin jumu'a da aka gabatar a masallatan jumu'a daban-daban a ciki da wajen kasarnan, shiri ne da Ammar Isah Nuhu Batagarawa ke shugabanta tare da taimakawar Basheer Journalist Sharfadi,**
**Shiri ne da yake da dimbin masu sauraro sannan zaku dinga jin halin da duniyar musulunci ke ciki a kowane mako ta cikin shirin, zaku iya samun wannan shiri da ma wadanda suka gabata a kowane lokaci a www.darulfikr.com**
**Domin daukar nauyi ko tallata hajar ku ta cikin shirin, ko kuma aiko da taku hudubar sai a tuntubi: 08035830253, 08066989773, 08149332007, dagamasallatanmu@gmail.com**
**http://facebook.com/masallatanmu.ng http://twitter.com/dagamasallatai**




## Yan Sanda Sun Kama Yan Shi'a Sama Da 50 A Abuja

Rundunar 'yan sandan Najeriya ta kama mabiyar Shi'a sama da 50 a Abuja babban birnin kasar a lokacin da suke gudanar da zanga-zanga.
'Yan sanda sun ce, sun kama mutanen ne bayan da zanga-zangar tasu ta koma kai hari kan fararen hula da ba su ji ba ba su gani ba.
Sanarwar da helkwatar 'yan sandan Abuja ta fitar ta bakin kakainta Anjuguri Manzah ta ce, sun kama mutane 52 mabiya Shi'a inda suka samu kwalaben bam din fetur a hannunsu, da ma duwatsu da suka yi amfani da su wajen kai wa jami'an 'yan sanda hari.
'Yan sanda sun harba harsashai sama da hayaki mai sa hawaye don tarwatsa masu zanga-zangar wanda hakan ya sanya wasu suka sami raunuka.
'Yan Shi'ar na Najeriya na zanga-zangar neman a saki shugabansu Ibrahim Elzakzaky da aka kama tun shekarar 2015 tare da matarsa.
'Yan kungiyar sun ce, an kashe akalla mambobinsu 2 a ranar Lahadin da ta gabata a yayin zanga-zanga a Kaduna....

Yan shi'ar dai sun bige da yin zanga-zanga da kuma tayar da tarzoma a tsakanin al'umma da kuma zzagi ga hukumomin tsaro da kuma jami'an gwamnati tun bayan rikicin ranar 12 ga December na shekarar 2015 wanda ya faru a garin Zaria wanda hakan yayi sanadiyar kame da kuma tsare jagoransu Mal. Ibrahim El-zakzaky,
Dama dai tun kafin wannan lokacin sun shafe tsawon lokaci suna karya dokar kasa yadda suke so tare da kafa nasu gwamnatocin a matakan kasa da jihohi,
Allah ya kyauta,

Rahoto: ***Muhd Habib Adam***



# Cikakken Tarihin Marigayi Sheikh Ja'afar Mahmoud Adam

## Menene Yasa Gwamnati Bata Saki Zakzaki Ba Har Yanzu ? -Nasir Ahmad Bawa

A fahimtata ina ganin abunda yasa bata sake shi ba (inyana Raye) watakila saboda ta saki Shugaban Biafara sai gashi daga baya ya cigaba da kafa Gwamnatin shi a cikin Gwamnatin Nigeria kuma ya cigaba da tada fitina : to La:alla wannan yasa ba a saki zakzaki ba kuma ya kamata Mutane su sani cewa Koda Ahlussunnah ne ya kafa Gwamnati a cikin Gwamnatin Nigeria wallahi Gwamnati bazata barshi ba, Dan haka bawai dan zakzaki Dan shia bane aka kama shiba : Zakzaki da kanshi ya tabbatar sun kama Dan Boko Haram a tattakin su na kano zuwa Abuja : suka cire Bom dindake jikin shi : Mai makon su Mika Bom din dashi Dan Boko Haram din a Hannun Hukuma : sai zakzaki dan ya nuna shima Hukuma ne sai yayi ma Dan Boko Haram din shari;a ya yafe mai yaki mika Bom din da Dan boko Haram din a Hannun Hukuma saboda bai yarda akwai Hukuma a kasar nan ba : to dan Allah ta yaya Hukuma zata kyale wannan ? Ko a iran wallahi kayi wannan Hukuma bazata kyale kaba...

Yan tawaye nawa kasar iran ta kashe ? Nawa ta Daure ?
Zakzaki ko wace jaha a nigeria yanada gwamnan daya kafa yanada sojojin shi na sama dana kasa dana ruwa don haka da Zakzaki da shugaban boko haram da shugaban Biafra duk babu wata gwamnati a duniya da zata kyale su, mu gayawa kanmu gaskiya ni inda za ayi shawarata sai ince a saki zakzaki saboda ai yaga aya babu wani tasirin da zaiyi yanzu in yana rayen kenan, koda yake ban sani ba ko gwamnati tana ganin idan ta sake shi zai zama kamar shugaban Biafra ne wanda daga sakin shi ya sake tada fitina,
Allah ya zaunar damu lafiya ameen.

Marubuci: ***Nasir Ahmad Bawa***





An haifi marigayi Sheikh Ja'afar Mahmoud Adam agarin Daura, a shekara ta 1962 (ko da yake wani lokacin yakan ce 1964). Marigayi Sheikh Ja'afar ya fara karatunsa na allo a gidansu, a wurin mijin yayarsa, Malam Haruna, wanda kuma dan uwansu ne na jini. Daga nan kuma sai aka mayar da shi wajen wani Malam Umaru a wani gari wai shi Koza, kimanin kilomita 9 a arewa da Daura, wanda shi ma akwai dangantaka ta jini a tsakanin su, wanda kuma shi ne musabbabin zuwansa Kano. Bayan sun zo Kano ne tare da wannan malami nasa, a shekara ta 1971 (ko 1972), sai suka zauna a makarantar Malam Abdullahi, wanda asalinsa mutumin jamhuriyar Nijar ne, amma yake zaune a unguwar Fagge a Kano. Tun kafin zuwansu Kano, tuni marigayi Sheikh Ja'afar ya riga ya fara haddar Alkur'ani mai girma, wanda ya kammala a shekara ta 1978...

Bayan da Malam ya kamala haddar Alkur'ani mai girma, kasancewarsa mai sha'awar ilimi, sai ya shiga makarantu biyu a lokaci daya a shekara ta 1980. Ya shiga makarantar koyon Larabci ta mutanen kasar Misra a cibiyar yada al'adun kasar Misra, (Egyptian Cultural Centre), sannan kuma ya shiga makarantar manya da ba su yi boko ba ta Masallaci Adult Evening Classes, tunda a lokacin shekarunsa sun wuce shekaru na primary, amma duk da haka a wannan lokaci shi ne mafi kankanta a ajinsu. Haka ya rika yin wannan karatu guda biyu: Waccan makarantar ya je ta da daddare bayan sallar isha'i, waccan kuma ta koyo harshen larabcin da yamma. Ya kammala wadannan makarantu a shekara ta 1983. Wannan kuma shi ya ba shi damar shiga makarantar GATC Gwale a shekara ta 1984, kuma ya kammala a shekara ta 1988...

A shekara ta 1989, malam ya sami gurbin karatu a jami'ar musulunci ta Madinah, a inda ya karanta ilimin tafsiri da Ulumul Kur'an, wanda kuma ya kammala a shekara ta 1993. Sannan kuma Sheikh Ja'afar ya sami damar kammala karatunsa na digiri na biyu (Masters) a Jami'ar Kasa-Da-Kasa Ta Afrika da take Khartoum, Sudan. Sannan kuma, kafin rasuwarsa, ya riga ya yi nisa wajen karatunsa na digiri na uku wato digiri da digirgir (PhD), a Jami'ar Usman Dan Fodiyo da take Sokoto...

Daga cikin malamansa na ilimi, akwai malaminsa na farko, mutumin kasar Masar, Sheikh Abdul-Aziz Ali al- Mustafa, da kuma Malam Nuhu a unguwar Dandago, wanda malam ya karanci ilimi fikihun malikiyya da wadansu littattafai na hadisi a gurinsa, da kuma Malam Muhammad Shehu, mutumin Lokoja, wanda Malam ya karanci nahawu da sarfu da balaga da adab a wajensa. Akwai kuma Sheikh Abubakar Jibrin limamin masallacin Juma'a na BUK, akwai kuma Dr. Ahmad Muhammad Ibrahim shi ma na jami'ar Bayero ta Kano...

Daga cikin malamansa na jami'a kuma, akwai Sheikh Abdurrafi'u da Dr. Khalid Assabt. Daga cikin karatuttukan da malam ya karantar da su, sun hada da tafsirin Alkur'ani mai girma, Kitabuttauhiid, Umdatul Ahkaam, Arba'una Hadiith, Kashfusshubuhaa t, Bulugul Maraam, Riyaadussalihiin, Siiratun Nabawiy, Ahkaamul Janaa'iz, Siffatus Salaatun Nabiiy.

Wasu daga cikin daliban malam sun hada da Malam Rabi'u Umar R/Lemo da Malam Sani Abdullahi Alhamidi Dorayi da Malam Abdullah Usman G/Kaya da Malam Usman Sani Haruna da Malam Ibrahim Abdullahi Sani da Malam Ali Yunus Muhammad da Dr. Salisu Shehu da Malam Shehu Hamisu Kura da Malam Anas Muhammad Madabo.

Kafin rasuwarsa, malam ya fara gagarumin aikin rubuce tafsirinsa a harshen Hausa a karkashin wannan cibiya ta (Sheikh Ja'afar Islamic Documentation Centre).

Marigayi Sheikh Ja'afar Mahmoud Adam ya rasu ranar juma'a 26/Rabii'u Awwal/1428 (13/04/2007) sakamakon harin da wadansu 'yan ta'adda suka kai masa, a daidai lokacin da yake jagorantar sallar asuba a masallacin Juma'a na Dorayi. Ya rasu ya bar mata biyu, da 'yaya shida, yayin da aka Haifa masa ta bakwai kwanaki 58 daidai bayan aiwatar da wannan kisan gilla a kansa. Dubun-dubatar mutane ne daga ko'ina cikin kasar nan suka halarci jana'izarsa, kuma an binne shi ne a makabartar Dorayi. Allah ya ji kan sa ya gafarta masa, ya saka masa da gidan aljanna. Amin

## Izala NHQ Jos Ta Kai Ziyarar Dubiya Ga Sheikh Madu Mustapha A Jihar Borno

Wakilan Shugaban Majalisar Malamai JIBWIS Na Kasa Sheikh Muhammad Sani Yahaya JINGIR Sunkawo Ziyara Ta Musamman Wajen Sheikh Modu Mustapha Maiduguri anan Gidan Sa Dake Cikin Birnin Maiduguri, Jihar Borno.

Sheikh Col Adamu Girbo Muhammad Rtd, Sheikh Aliyu Bara, Ustaz Dauda Kaloma Suka Wakilci Shugaban Malamai Na Kasa.

Bayan Sun Isar da Sakon Sheikh JINGIR kuma Sunyi Mishi Adu'a Ta Musamma Akan Allah Yakara Mishi Lafiya Kuma Jinyar da Yayi Yasa Kaffara Ce Agareshi.
Shugaban Malamai Na Jihar Borno Sheikh Muhammad Musa Shi Ma Ya Nuna Farin Cikinsa da Godiyar sa da Wannan Ziyarar ta Musamman....

A nasa Jawabin Sheikh Modu Mustapha Yayi Farin Ciki da Wannan Ziyaran Na Yan Uwan TakaTa Addini kuma Ya Nuna Matukar Godiyar Sa Ga Shugaban Majalisar Malamai Na Kasa Yadda Yake Numa Mishi Soyayya, Kuma Yayi Adu'a Ta Musamman Kamar Yadda Addini Ya Hadamu Yesa Mu Dauwama Acikin sa Kuma Yahada Fuskokin Acikin Jannatul Firdaus.
Sheikh Modu Mustapha Maiduguri Shine Mataimakin Sakataren Malamai JIBWIS Na Kasa, Wanda Yayi Fama da Jinya a Kwanakin Baya Wanda Yanxu Alhamdulillah Yasamu Lafiya.
Allah Ya bada Ladan Wannan Ziyara kuma Yahada Kan Malamai Mu Akan Gaskiya, Yabamu Lafiya da Zaman Lafiya
Rahoto: ***Hassan Auwalu Ya'u***



# SASHEN TALLA

## Izala Reshen Jihar Kaduna Ta Mika Sakon Ta'aziyya

A Madadin Shugaban Kungiya Alh Muhammadu Tukur Isa,
Da Director Agaji Alh Adamu Ibrahim
Da Shugaban Majalisar Malamai Sheikh Aliyu abdullahitelex da sauran 'yan Majalisar sa,Suna mika sakon taziyyar su ga daukacin Al'ummar T/Wada da iyalan Alh Abdullah Indagi Wanda Allah yayi masa rasuwa a cikin wannan makon. Allah ya gafarta ma sa, jinyar da yayi Allah yasa ta zame ma sa kaffara.
Muna rokon Allah ya gafarta ma sa.
Iyalan sa Allah ya basu ladan hakurin rashinsa, abinda ya bari, Allah yayi masu albarka.
Allah ya sa ya huta.

## Izala Zata Gabatar Da Wa'azi A Jihar Kaduna

A Madadin Shugaban Kungiyar Izala ta Jahar Kaduna Alh Tukur Isah
Shugaban Majalisar Malamai Imam Aliyu Telex ZARIA
Director Agaji na Jaha Mal Adamu Ibrahim
Da Mataimakan su Suna farin cikin gayyata 'yan uwa zuwa gagarumin wa'azi na Jaha kamar yadda ta saba agarin Kafin Allah gaba a Karamar Hukumar Ikara. Tare da bude Makaranta awannan centre.
Ranar Asabar da lahadi:
25/04/1439 (13/01/2018)
26/04/1439 (14/01/2018)
Ana sa ran halartan Manyan Malamai da Alarammomi zasu halarta,
Allah ya bada Ikon Halarta.

## Izala NHQ Jos Zata Gabatar Da Wa'azin Kasa A Gombe

Kungiyar Izala NHq Jos Tana Farin Cikin Sanar da Al"umar musulmi Ahalussunnah zuwa wajan gagarumin **wa"azin kasa da kasa a Jihar Gombe a Karamar Hukumar Kumo a ranakun Asabar da Lahadi 26 - 27/4/1439 H, 13 - 14/1/2018 M,**

Kamar yadda aka saba Allah yabada ikon zuwa ameen,

## Izala Zata Gabatar Da Wa'azin Walima A Jihar Kebbi

Shugaban Kungiyar Izala na Warra karamar hukumar Mulki ta Ngaski Alhaji Na Allah Mai mai da Honourable Garba Hassan Shugaban karamar hukumar Mulki ta ngaski A madadin Qungiyar Jama'atu Izalatil Bid'ah wa'iqamatus Sunnah reshen karamar hukumar Mulki ta Ngaski suna farin Cikin gayyatar Yan uwa Musulmi zuwa wurin gagarumar walimar da za a gabatar ta samun Nasarar Chairmn Ngaski
Wanda za'ayi Kamar haka:
Rana :Lahadi 7-1-2018
Lokaci :karfe 8:00 na Dare.

# DAGA KASASHEN WAJE

## Muhadarori Guda Biyu Na Musamman A Abuja

Babban Malamin nan Dr. Bashir Aliyu Umar zai gabatar da Muhadarori na musamman a birnin tarayya Abuja masu taken:

*HAKKOKIN ZAMANTAKEWAR AURE*

Muhadhara ta farko

Talata 28/4/1439-16/1/2017
Maudhu'i: hakkokin zamantakewar aure
Lokaci: tsakanin magrib da isha'i
Wuri: Masallacin juma'a na Annur IBB way Wuse 2 Abuja

Muhadhara ta biyu

Laraba:29/4/1439-17/1/2018
Maudhu'i: hakkokin zamantakewar aure
Lokaci: tsakanin magrib da isha'i
Wuri: Masallacin juma'a na Annur da keibb way Wuse 2 Abuja
Sanarwa: ***Diya'ul Haqq Muhd***

## An Soke Hukuncin Sakin Musulmai 7 A Kasar Jamus

A Ranar Alhamis dinnan Babbar kotun kasar Jamus ta soke hukuncin kotun dake birnin Wuppertal ta dauka a shekara ta 2016 na sakin wasu Musulmai bakwai da aka samu da laifin sanya kaki na agajin gaggawa da kuma umarni da kyakykyawa da hani da mummuna, sannan suna kula da harakokin shari'ar Muslunci a tsakanin al'ummar Musulmi mazauna garin Wuppertal na tsakiyar kasar.
A watan Satumban 2014 ne aka samu Musulman guda bakwai sanye da kayan kaki wadanda aka rubuta "Yan sandar Chari'a" a samansu suna gudanar da sintiri a saman titunan birnin na Wuppertal mai kunshe da Muslmi da dama, inda suke tare matasan Musulmi suna gargadinsu kan su kaurace wa shan barasa da zuwa gidajen rawa da na wasanni da na caca. Wannan dai shine dalilin da yasa aka garkame wadannan bayin Allah, Allah ya kyauta.

## An Kashe 'Yan Kasar Iran A Syria

An sanar da cewa 'yan kasar Iran da ke yakin kare hukumar kasar Siriya 7 sun rasa rayukan su.
Kamar yadda kanfanin dillancin labaran kasar Iran Tesnian ta sanar anyi jana'izar 'yan "Fatimiyyun" da "Zeynebiyyun" da su ka rasa rayukansu a rikicin Siriya a garin Kum .
A wa ta majiya da ba'a tabbatar ba, a rikicin na Siriya an kashe 'yan kasar Iran har dubu 2 da 400.
An bayyana cewar 'yan Afganistan da su ka shigo Iran su ka hada Fatimiyyun Brigade da kuma 'yan Pakistan da su ka kirkiro Zeynebiyyun brigade na baiwa gwamnati Bashar Asad a Siriya gudunmowa da dukkan karfin su.

## Mahaddata Alkur'ani Mai Tsarki Na Kara Yawa A Kasashen Turai

Tun bayan fara Rainon Yara tare da ganin sun haddace Alku'ani Mai Tsarki a masallacin Salimiye na Amsterdam Babban Birnin Kasar Holan a shekarar 2010, ya zuwa yanzu yara matasa sama 20 ne suka Khattama haddar tasu.
Limamin Masallacin na Salimiye da ke Amsterdam Hafiz Ahmad Kaya ya bayyana cewa, nan da wani lokaci za su aiwatar da hanyoyin Koyar da Haddar a Sauran manyan masallatan Kasar ta Holan.
A shekarar da ta gabata wani yaro mai shekaru 14 Amir Kurban ya kammala haddarsa a Masallacin na Salimiye ya ce, abu ne mai dadi da shauki mutum ya haddace Alkur'ani Mai Tsarki.
Limamin Masallacin Juma'a na Mevlana da ke Amsterdam Hafiz Abdullah Kayın ya ce, suna da burin kafa irin wadannan makarantu na Haddar Alkur'ani a Kasashen Turai baki daya.
Akwai dalibai 814 da suka hada da mata 560 da suke karatu a cibiyoyin Haddar Alkur'ani na kasashen Turai baki daya karkashin kulawar Hukumar Diyanet ta Turkiyya da kuma Kungiyar Al'Umar Musulmi ta IGMG.

## Saudiyya Ta Janye Dokar Muharrami Ga Mata 'Yan Sama Da Shekaru 25

Kasar Saudiyya ta bayyana cewar za ta fara baiwa mata 'yan sama da shekaru 25 damar shiga kasar ba tare da muharami ba.
Shugaban hukumar yawon bude idon kasar Omar Al- Mubarak ya bayyana cewar domin kara habbaka lamurkan yawon bude idon, kasar Saudiyyar za ta janye dokar muharrami ga mata da su ka fiye shekaru 25.
Mubarak ya kara da cewa visar da za'a baiwa matan ba za ta wucce na kwanaki 30 ba.
Wannan matakin nada nasaba ga irin matakan da yarima Muhammed Bin Salman ke dauka domin bunkasa tattalin arzikin kasar ta hanyar habbaka fannonin bude ido, da kuma yin kwaskwarima ga tsattsaurar ra'ayi.
Baya ga garin Makka da Madina za'a kuma baiwa baki 'yan yawon bude idon damar yin aiki a fadin kasar Saudiyyar.
Za'a kuma fara gina wani katabaren gurin shakatawar kasa da kasa a cikin wasu hamada 50.
Haka kuma ana hasashen za'a kammala ginar yankin 'yancin da za'a dinga amfani da dokar kasa da kasa maimakon shari'ar musulunci a shekarar 2022 a kasar.

## Saudiya Tace Tana Kan Bakanta Na Goyon Bayan Palasdinawa

Sarkin Saudiya Salman bin Abdulaziz ya tattauna ta wayar tarho da shugaban Falasdinawa Mahmud Abbas inda ya jadadda cewa, kasarsa za ta ci gaba da goya wa Falasdin baya.
Kamfanin Dillancin labarai na Saudiyya SPA ya ce, Sarki Salman ya bayyana wa Abbas yadda Saudiyya ba ta sauya halinta ba game da Falasdin.
Sarkin ya ce, Saudiyya tana ci gaba da aiyukan kare hakkokin Falasdinawa tare da ganin an kafa 'yantacciyar kasar Falasdinu.
Salman ya kara da cewa, zai ci gaba da aiki da hukuncin Majalisar Dinkin Duniya wajen ganin an kawo karshen matsalar falasdin da Isra'ila.

## Sojojin Isra'ila Sun Kama Palasdinawa 11

Kamar yadda rundunar sojan Isra'ila ta sanar a hare-haren da ta kai a Zirrin Gaza jiya da dare ta kame Falasdinawa 11 inda ta zarge su da aikata laifin ta'addanci.
Sojojin Isra'ila dai na yawan kame Falsdinawa a Zirrin Gaza da gabashin Qudus da su ke mamaya ta zarginsu da laifuka daban-daban.
A gidajen yarin Isra'ila an bayyana cewar akwai Falasdinawa dubu 7 da su ka hada da yara 300 a yanzu.
Sojojin Isra'ila sun kame wa su Falasdinawa 11 da sunan aikata laifin ta'addanci
Kamar yadda rundunar sojan Isra'ila ta sanar a hare-haren da ta kai a Zirrin Gaza jiya da dare ta kame Falasdinawa 11 inda ta zarge su da aikata laifin ta'addanci.